# JIYA DA YAU: A DUNIYAR MAKADAN FADA

GABATARWAR:

ALHAJI IBRAHIM MUHAMMED

(*DAN MADAMIN BIRNIN MAGAJI*)

*KWAMISHINAN KASAFIN KUDI DA TSARE-TSAREN TATTALIN ARZIKI NA JAHAR ZAMFARA*

***birninbagaji4040@gmail.com***

# GABATARWA

- **Tsakure:**
- **Kida da Waka**
- Wakar baka ta gargajiya
- Wakar baka ta zamani
  - **Kasar Hausa.**
  - Sarauta a Kasar Hausa
  - Sarki a Kasar Hausa.
  - Fada a Kasar Hausa
- **Makadan Fada A Jiya.**
- Kayan Kidan Mawakan Fada
- Wakokin Fada
- Muhallin Rera su
- Tubalin ginin Wakokin Fada
- Roko
- Habaici
- Zuga
- Raya Harshe
- Zambo

# .....GABATARWA

- **Makadan Fada A Yau**
- Wakokin Makadan Fada  a yau
- Muhallin Rera Su.
- Kayan Kidan Makadan Fada a Yau
- Tubalin Ginin Wakokin Fada a Yau.
- **Kammalawa**
- Matsalolin Mawakan Fada Jiya da Yau.

- Rataye na 1.
- Misalin Wakokin Fada Jiya da Yau

- Rataye na 2
- Sunayen wasu daga cikin mawakan fada jiya da yau

# JIYA DA YAU: A DUNIYAR MAKADAN FADA

**Tsakure:**

A duk lokacin da ake son ganin tarihin wata al'umma, ci-gabanta da matsalolinta ana komawa ne kai tsaye ne kan adabinta, ta nan ne ake fahimtar al-adunta da dabi'unta. Makadan fada sun zama wani kundi na adana tarihin Masarauta da Sarautun kasar Hausa da Zamantakewa da fadi-tashi da gwagwarmayar da ake yi a fada. Makadan fada suna shiga irin ta Sarakai haka abin kidansu sun kevanta ne da wakokin fada. Yau da gobe ba ta bar kome ba. Kwanci tashi sauyi ya zo a duniyar mawakan fada aka bar jiya aka wayi gari a yau da muke saboda yanayin da zamani zo da shi ta sanadiyyar cudanyar da al'ummar kasar Hausa ta yi da baki. Wannan ta sa aka sami karin Turakan wakar fada bayan Turakun farko. Sannan an sami kari kan muhallan da ake rera wakar gargajiya a yau.

# GABATARWA

Waka tana cikin makarantar farko ta Bahaushe wanda cikinta yake koyon ilimi na rayuwar yau da kullum. Wannan takarda an yi ta ne kan mawakan fada na jiya da na yau inda aka raba ta zuwa gida biyar.

Kashi na farko takardar ta kalli kida da wakar baka ta gargajiya da ta zamani

A bangare na biyu takardar ta kalli kasar Hausa, yanayinta da al'ummarta da al'adunta da sarautarta kama daga sarki, fada da sarautar kanta.

Kaso na uku a takardar an mayar da hankali ne kan jigon takardar wato makadan fada a jiya da yau a karkashin wannan an duba al'ada da dabi'a da yanayin mawakan baka na fada a jiya yadda suke aitawatar da wakokinsu da da kayan kidansu da tubalan da suke amfani da su don tayar da wakar fada a karkashin kowanne an kawo misali don karfafa hujja

# .... GABATARWA

A kaso na hudu an duba wakar fada a yau ne inda aka kalli mawakan baka na fada a yau da yadda suke gudanar da wakokinsu tattare da misalan wakokin.

A kaso na biyar takardar ta kammmala da diba duniyar makadan fada tare da kawo shawarwari. Rataye da manazarta sune suka zo a karshen takardar.

# KIDA DA WAKA:

**Kida da waka wasu muhimman al'amura ne wadanda kowacce al'umma ke amfani da su ko dai don isar da** wani sako ko don nishadi. Haka yake gun Bahaushe kida da waka yana cikin adabinsa.

Funtua (2010:65) yace waka takobi ce ta al'ada. Haka kuma waka wata kyakkywar hanya ce ta adana tarihin al'umma.

# .....KIDA DA WAKA:

Umma, (2005: 100) Ta bayyana wakar baka da "ita ce wadda ake yin ta a ka, a aiwatar da ita da ka, ta hanyar rerawa ba karantawa ba".

Dumfawa ya ce "Waka na daya daga cikin dadaddan hanyoyin Hausawa na koyar da ilimi a cikin nishadi. Waka ita ce hanyar koyar da al'umma tarbiyya da kuma dabarun zaman duniya gabanin zuwan Musulunci da kuma wayewar kai ta hanyar karatu da rubutu".

# GARGAJIYA:

- Gargajiya na nufin wani abu da can da aka gada tun iyaye da kakanni, wato wani abu da ya riski da.

**Kasar Hausa**

Umar, (1999:12) Kasar Hausa kasa ce mai fadin gaske wadda take kunshe da al'ummu mazauna wurare daban - daban a cikin manya da kananan birane da garuruwa bisa dukkan alamu, Hausawa su ne  mazaunan farko, inda daga bisani suka gaurayu da wasu al'ummomi, bayan da suka shaku da juna suka zama abu daya".

Malumfashi da Ibrahim, (2014:10) Sun ce "samuwa da ginuwar kasar Hausa ya faru ne lokacin da mutane suka dawo daga rakiyar yawo da farauta da kuma yaki domin neman abinci da sauran abubuwan tafiyar da rayuwa".

# SARAUTA A KASAR HAUSA

Sarauta a kamusun Hausa (2006:350) an bayyanata da shugabanci, musamman irin na gargajiya.

- Kalmar Sarauta kamar yadda Umar (1999:14) ya bayyana tana da ma'anoni daban-daban. Amma dukkan ma'anoni za a ga sun ginu ne a kan wannan shika-shikai guda ukku, wato shugabanci da mulki da kuma iko. Shugabanci shi ne yi wa jama'a jagora a harkokinsu na zaman tare, Mulki kuwa ya danganci yawan jama'ar da mutum ya shugabanta, da rayuwarsu, da kuma girman muhallin da suke zaune a ciki da karfin jagorancin da yake iya yi masu, sukunin bayar da umurni da hani da tsaro kuwa shi ne iko.

# .....SARAUTA A KASAR HAUSA

- Alhassan da wasu, (1980:12) Ya ce Sarauta ita ce shugabantar jama'a don kiyaye addininsu da tafiyar da harkokin siyasarsu, da samun hanyoyin jin dadin rayuwa masu kyau da kyautata hanyoyin tattalin arzikinsu da duk wasu al'amura na yau da kullum, musamman da abin da dan'adam zai bukata na inganta rayuwarsa.

# SARKI

Sarki jagora ne na mutane mai ikon gudanar da mulki a hannunsa. Shi ke zartar da kowane hukunci a kasarsa amma wasu lokutan yakan nemi ra'ayin mashawartansa.

Gaya, (2010:65) Ya nuna cewa samun zama Sarki ya tattara ne a kan hanyar gado da nuna jarumtaka da zaben cancanta. Haka addinin Muslunci da ya shigo ya tabbatar da zaben cancanta dangane da tsoron Allah da sanin Ilimin addinin Musulunci da kuma adalci.

# WASU SARAKUNAN KASAR HAUSA











# FADA

- Fada kamar yadda Isma'il, (1996:1) ya ce "wani waje (wuri) ne na musamman da ake taruwa domin tattauna muhimman abubuwa a gaban Sarki dangane da harkokin yau da kullum tare da shawarar yadda za'a vullowa wani abu da ya taso tare da neman hanyar da za'a magance shi.



# MAKADAN FADA:

Makadan fada sune wadanda ke aiwatar da wakokinsu ga wani Basarake guda a matsayin Ubangidansu ba tare da sun hada shi da wani ba, in kuwa sun hada din to sai da izininsa ko wani amininsa kuma da sharadinsa. A duk lokacin da wani Basarake ya riki wani Makadi a matsayin mawakinsa na fada to fa cin wannan makadi da shansa da suturarsa da muhalli da dawainiyarsa duk sun rataya ne kan wannan ubangidan nasa. Da yawa daga cikin wadannan mawakan sun gaji wannan ne daga wajen iyaye da kakanninsu

A wasu lokutan, makadan fada na daina yi wa Basarake kida saboda wani dalili na musaman, ko dai don gaza daukar








# …..Sarki

nauyinsu ko canza ubangida ko rasuwar wanda aka yi wa kidan ko kuma ra'ayi. Misali, Makada Aliyu Dandawo Shuni ya fara da Ardon Shuni Mamman ya kare da Sarkin Yauri Abdullahi Abarshi.

Shi kuma Alhaji Musa Dankwairo ya gaji yi wa Sarkin Kayan Maradun waka daga Babansa; Usman Dankwanaga, anan kuma ya tsaya sai dai ya je Balaguro ya dawo gida Maradun.

# Wakokin Makadan Fada

- Kafin Hausa, (2002):241) Ya ce wakokin Sarauta wakoki ne da suke cike da hikimomi da fasaha da nuna zalaka irin ta al'ummar Hausawa. Sannan kuma suna dauke da salo iri-iri na Sarrafa harshe kamar su kirari ko Karin Magana da karangiya da dai sauransu da abubuwa masu kara nuna gwanintar harshe.

# MUHALLIN RERA WAKOKIN FADA

- A fada
- A wajen rangadi
- Wajen taron daba
- Bukukuwan Sallah
- Bikin ‘Ya’yan Sarki
- Nadin Sarauta
- Lokacin Kai gaisuwa a kofar gidan Basarake.

# TUBALIN GININ WAKOKIN FADA

- Zambo
- Tarihi
- Zuga
- Yabo
- Zamantakewa
- Al'ada
- Raya harshe
- Roko
- Habaici
- Kirari

# ZAMBO

Bello(1976:31)Ya ce "zambo dai shi ne na fadin wani mugun abu ga mutum a takaice zambo dai shi ne kishiyar yabo." A kusan dukkan lokuta, wadanda aka yi wa wannan Zambo suna gane da su ake, ko kuma al'umma na iya fahimtar da su ake, kila saboda yadda aka bayyana kamaninsu a cikin zambon:-

# .....ZAMBO

**Misali:-** A cikin wakar Alh. Musa Dankwairo Maradun da ya yi wa Sarkin Tsafe dake Jahar Zamfara, watau Marigayi Yandoton Tsafe, Alh. Aliyu Maitaken "shirya kayan Fada Maigida Tsafe" yana cewa
Kyawon dan Sarki Talatin,
Dan Sarki duk yay yi sittin bai gadi gidansu ba ta bace mai, Sai bidat Jalli, ai tugun Jakkai,
A samu na shan dawo kar a lalace".
A wani baitin kuma yana cewa
"Baya wargi da Moro na Abubakar,
Tunda wargi da tallaka, aibune,
Gaka kahishi iko ya rena ka".
(Karin bayani).

# .....ZAMBO

- Suna iya karkatawa su yi wa wani Sarki Zambo, ko dai saboda yana jayayya da Ubangidansu ko kuma yana yi masu rowa. Misali a cikin wakar Sarkin Gabas Na Mafara (Jahar Zamfara) Marigayi AIh. Shehu, wadda Malamin waka,, Marigayi Sa'idu Faru ya rera masa

Mai taken, "Ki garaje Uban Shamaki Shehu, Dan Muhamman Sarkin rikon Taro" Yana cewa
"Biyat Shehu duk tahi bin rangama, Wadanga Sarakunan Zamani,
Yayin Gimbiya masu guntun nadi,
Icce da kogo ina za'a kyautar kirki"
(Karin bayani).

# TARIHI

Sanin tarihi abu ne mai muhimmancin gaske domin ta nan ne ake sanin abin da ya gabata domin gyara wanda zai zo. Kowanne abu yana da tarihi yadda ya kafu. A cikin waka ana iya sanin tarihin kafuwar Sarauta ko al'ummarta.

A fagen Tarihi kuwa Makadan Fada sun yi kokari matuka na fitowa da Asalin Masarauta ko Basaraken da suke yiwa waka. Alh. Musa Dankwairo Maradun a wakarsa ta Bai kasa ba, bai gaza ba, wadda ya rerawa Marigayi Mai Martaba Sarkin Daura, Alh. (Dr) Muhammad Bashar, yana cewa:

- "Nai Tambaya a Najeriya ina asalin Hausa Bakwai sun ce birnin Daura,

# ....TARIHI

kasar Nijar da niyyi tambaya ina asalin Hausa Bakwai, Sun ce Birnin Daura,
kasar Kamaru da niyyi tambaya ina asalin Hausa bakwai, Sun ce birnin Daura.
daga Sakkwato har Argungu sun san Birnin Daura, birnin tarihi ne" (karin bayani).





# ....TARIHI

Haka ma, Marigayi Sa'idu Faru a cikin wakarsa ta Sarkin Kudu/Sarkin Musulmi Marigayi Alh. Muh'd Maccido Maitaken "Kana shire Babban Yanruwa, Na Bello Jikan Danfodio, 'yana Cewa
"Diba Kafakka zuwa bisa hannuwa,
Zaman Shehu na ba wata za'ida,
Sarkin Musulmin wata ran kake,
Da imani da mu'ijjiza na nan ga Mallam Maccido,
Tun ga Alu Mai Saje Nijjiya" (Karin bayani).





# ….TARIHI

Alh. Musa Dankwairo Maradun yana bayar da tarihin garuruwa da sunan Sarakunansu da ma sunayen Sarautar garuruwan da ke tsakanin Sakkwato zuwa Kaduna, tun daga Shuni har zuwa Rigachikun, a cikin wakar mai dubun Nasara garnakaki Sardauna.

"Amadu ya zo Hausa, za shi gida nai rannan, Yansanda, Yandoka da Ministocin Gohe

# ....TARIHI

- Duka Jama'a sun taru, suna yi mai bankwana Suna ta Rokon Allah" Wada kazzo da lahiya Allah kaika lahiya ka sabka zai kyawo domin girman Manzo"
- "Hatta Ardon Shuni, Mamman yai tariya tai Yana ta rokon Allah wada kazzo da lahiya Allah kai ka lahiya ka sabka zakkyawo domin Girma Manzo"
- (Karin Bayani)





# ZUGA

- Gusau, (2002:302) Zuga tana dauke da wasu kalmomi ne da ake amfani dasu, a koda wani mutum a ciccika shi, a nuna fifikonsa kan wasu" Alh. Aliyu Dandawo Shuni a wakarsa ta "Mai Yauri Bangon Duniya wadda ya yi wa Marigayi Mai Martaba Sarkin Yauri (Jahar Kabi) Alh. Abdullahi Abarshi yana cewa:
- "Ba a haye maka sai in ka yarda,
- Abdu kahi Madwacci dwaci, kahi Guba in an ka Zure ma.
- Kahi wuta Zahi Dan Mamman, wanda Allah yabba yaddak ka yahi bin shanu ayi ikko, kafi Gwanja, Kafi Kano.
- Abdu ko Masar sai dai ayi tono ruwan zuma ba lasar dauda".

# YABO

- Gusau, (2002:301) Ya bayyana yabo da shi ne "Ambaton kalmomin sambarka da nufin nuna amincewa da hali ko wani abin da mutum ya yi nagari "Mawakan Fada suna amfani da yabo matuka cikin wakokinsu don su nuna nagartar wanda suka yi wa waka".

# ....YABO

Marigayi Ibrahim Narambada, a cikin wakar Sarkin Gobir na Isa, Amadu na daya mai taken "Amadun Bubakar gwarzon yari dodo na alkali" yana cewa:

"Dokin nan da kabbani
Ko da uban mutum assarki
Iri nai yakan Hausai".

Makada Maidaji Sabon birni, yana cewa a cikin wakar Sarkin Gobir Umaru na Sabon birni, gwarzon Galadima, ya ci fansa, uban yari babban barga Na bango".

“Zamaninka dan Inna mun yi saibi
mun sha hurar Nono, mun ci kalwa
mun hau dawakayye mun yi zama”.

# ....YABO

Alh. Musa Dankwairo Maradun a cikin wakarsa ta Batakura Kabrin gaba, wadda ya yi wa san Kano, Alh. Ado Bayero ya kwatantashi da Aljannar duniya saboda tsananin Yabo".

"Aljannat duniya
dan Abdulkadir Sarki Ado
na tareda kai ya lilwanta
ruwan wankin dauda ne"




# ZAMANTAKEWA:

- Zamantakewa na nufin “zaman tare wanda kan jawo shakuwa” kamusun Hausa (2006:489). Dumfawa, (2010:83) Ya ce zama a tsakanin jama’a akwai yadda ake son ya kasance.

# AL'ADA

- Al'ada tsarin rayuwar al'umma ne baki daya. ita ce baki dayan fasahar wannan al'umma na abin da suke aikatawa mai kyau ko akasin haka. Bahaushe mutum ne mai tsantsar riko da al'ada, ba kuwa inda ake aiwatar da al'ada da riko da ita kamar fada. Wannan kila ma shi ne ya sa mawakan fada suke da riko da al'ada saboda siffatuwa da fada.

# .....AL'ADA

- A cikin wakar marigayi, sarkin burmin Bakura Yusuf III wadda marigayi makada Abdun Inka Bakura ya yi masa (Mai Bakura jikan Amadu) yana cewa:
- "Dan sarkin da bai yi sarki ba
- bai san duniya da dadi ba
- don bai sha hura da nono ba
- bai ci tuwo da nama ba
- ko da ya ciyo abincin bai wuce **hocen** sule cikin **tabsakada** ko ga **miyar lalo**, ko agalbe bakuru)"

# RAYA HARSHE:

- Harshen Hausa, harshe ne da yake da wadatattun kalmomi wadanda ake amfani da su wajen gina waka don fito da fasaha da zalaka da azanci a cikin waka. Makadan fada suna sahun gaba wajen amfani da irin wannan azancin. Akwai rumbunan kalmomi da aka same su kebantattu da Mawakan fada kawai ke amfani da su.

# .....RAYA HARSHE:

Makadan Fada a Jiya sun yi fama sosai wajen raya harshen Hausa ta hanyar salon Magana da saka wasu kalmomin da suka kara bunkasa harshen Hausa. Misali, Saidu Faru a cikin wakarsa ta sarkin Kiyawan K/Namoda, Alh. Abubakar (Gwabron giwa na Shamaki, baba uban gandu) Ya jero wasu kalmomi masu sarkarkiya ga Bahaushe domin ya kara wa harshen Hausa haiba.

"Abu Baban Shamaki na Jekada,
Dangalin Gabas Na Issau Dan Mudi
kashi' tahi giggilme, kargage
farat fatsa cinki sai ga Mai kararrin Kwana,
"A ciki, a kwan rirrikar Mutun za shi garin Kewa".



# ROKO:

Makadan fada a Jiya suna rokon uwayen gidansu, ko a fakaice, ko a baiyane. Misali, Saidu Faru a cikin wakar Sarkin gabas na Mafara, Alh. Shehu (Koma shirin daga na Mu'azu) yana cewa:

"Daudu kullum mafalki ni kai Sabo
Shehu ya ba ni doki da kayanai
Danda hwari biyat wanda an nan haka
Inda liman Kabi zai Massallaci".

Shi kuwa Marigayi Salihu Jankidi Rawayya yana cewa a cikin wakar Sardaunan Sakkwato, Sa Ahmadu Bello (Sardauna zaki hana ay wargi).

"Shantali Maganar Dokina nai.
har na kahwa turke gida na"

Alh. Dankwairo Maradun a cikin takensa na dan Amadu Tsayayye da ya rera wa Sarkin kayan Maradun, Marigayi Alh. Muh'd Tambari yana cewa:

"Muhammadu sarki ka kai ni Makkah Amma hwa da kuddinka ba da nau ba".

# HABAICI:

Adamu, (2008:130) Ya ce habaici shi ne, wasu maganganu ne da ake fada a fakaice don ratayawa wani mutum ba tare da bayyana mutumin da ake nufi ba kuru-kuru ba. Amma shi wanda ake nufi wani lokacin da wuya ya gane abin da ko wanda ake nufi da shi."

A cikin wakar shirya kayan fada Maigida Tsafe wadda Alh. Musa Dankwairo ya rerawa, Yandoto Aliyu yana cewa"
"Maigirman kai bai kyau da hula
Sai dai ya yi malhwa ta hi umfani".
A ciki yana kuma cewa:
"Na rena burodi mai kumburin banza
Na saye na gani bai yi abki ba
Burodi mun gane cikinka iska ne".

A cikin wakar Salihu Jankidi ta san Kano, Alh. Sanusi I, (Arziki ya yi kai as sarki) Yana cewa"
"Rabbana ya yi ma taimako
Shi Ya karya maza sun  taushi
Mai Tsammani Ya Firgita.
Ya Zamo bana Kamar bayannan
Maitakama da katon Nadi"
(Wane na?)

# KIRARI:

Kirari shi ne kokarin yabo da kwarzantawa da nuna bajinta a kan yi wa mutum tuni da kakanninsa ko wani jarumi ko wani fitacce.

Ibrahim Narambada yana cewa a cikin faifansa na gogarman tudu jikan Sanda ta Sarkin Gobir Na Isa Amadu I yana cewa:
"Amadu dibi mazan gaba Dibi na baya
Ka diba dama, ka diba hauni kasan jama'agga da anan kauye da birni ba su da jigo sai kai
Madi bai kai ga zuma ba Ko wal lasa shi kahwadi
Kwando wake bai kai ga daman gero ba
Wane ku dangana tun ga iyaye Ba duk dan sarki ba ka samun sarki

# ....KIRARI:

Shi kuwa Sa'idu Faru a wakarsa ta sarkin yakin Banga Saleh (Gwabron giwa uban Galadima dan Sambo ginshimi) Yana cewa:
"Kwasau taron da Mun kazo Sakkwato
Mun daddaki ka
Don bamu da haushin kidi na kowa
Yau ko Isa ko Gummi
Ko da Gurso da shi da Jankidi
Yau Sun gaida rungumi
"Ga sarkin Kano da sarkin Daura Sun Kammale diya".
Marigayi Salihu Jankidi Rawayya a cikin baitin kirarin da ya yi wa Marigayi Sir. Ahmadu Bello (Sardaunan Sakkwato) ya dangata shi da Manzon Rahama (SAW) cikin wakarsa ta Amadu kara shirin duniya".
"Asalin Ahmadu Sardauna Bello
Tun daga ya Rasulullahi
Dab bisa Fadima har Ahsanu
Shehu Nizami kuma da Sunusi Muntada
Ga Yasi har da Musa Jokolo
Ukuba, Ilyasu, Abdullahi, Sibdiyyu
Abdussamadi, Nasiranu, Haruna,
Ayuba, Salihu, Usmanu, Muhammadu Bello
Abubakar Mai Rabah, Ibrahimu
kaji Salsalar Ahmadu Bello Sardauna Hakkun"





# MAWAKAN BAKA NA ZAMANI:

Bilkisu (2013:11) Ta ce wakokin baka na zamani su ne wakokin da aka samu sauyin rerawa, aka sami sauyin kayan kida daga wakokin baka na gargajiya suka sauya zuwa sabuwar hanya ta zamani, kamar mandiri da fiyano da kayan kidan disko.

Wadannan wakoki sun sami karbuwa wajen al'umma cikin kankanin lokaci.

# Makadan Fada a Yau:

- Bahaushe ya ce "kowa ya dade zai ga dadau haka yau da gobe kayan Allah" wannan sauyi ne ya sauyawa mawakan fada daga waccan duniyar ta gargajiya zuwa sabuwar duniya inda a wannan duniyar aka sami wasu sauye - sauye na zamani. Inda duniyar makadan fada ta karbi sauyi sakamakon shurewar lokaci sannan da bakin al'adu wadadanda sukayi tasiri. Makadan fada na wancan lokacin Allah ya amshi kayansa,  magadansu ko halifofinsu ba su dau hanyar su ba, ko da kuwa sun dauka ba su yi tasiri ba. Kwatsam sai Allah ya kawo makwafinsu matasa ko da ba su zama su sak ba to kuwa sun debo wani abu nasu. Sun dauka daga inda suka tsaya suka ci gaba daga nan.

# .....Makadan Fada a Yau:

A baya, mawakin fada kan dauki sarki guda ya sa shi gaba matsayin Ubangidansa wanda zai jibanci dukkan lamurransa, sabanin mawakan baka na zamani a yau. Kowanne mawaki kan bushi iska ya wake kowanne Sarki haka lokaci guda kuma ya wake duk abin da ya so, hakama yana da ‘yancin shiga kowanne jigo ya yi wakarsa.

A yau cikin mawakan baka na zamani babu wani mawaki da za a nuna a matsayin mawakin fada zalla. Sai dai cikinsu akwai wadanda suna da wakokin da suka yi wa sarakai fiye da kirge.

Shigar mawakan fada wata alama ce da ke nuna lalle wannan mawakin fada ne. Mawakan kan yi shigar manyan kaya da rawani don siffantuwa da kamala. A yau, akwai bambaci sosai domin kana iya ganin mawakin yanzu cikin manyan kaya kafin anjima a gan shi a tsuke.






# MUHALLAN RERA WAKOKIN FADA A YAU:

Duk wadancan muhallan da makadan fada ke bi wajen rera wakokin Fada a jiya mawakan fada a yau suna amfani da su sai ma karin wasu hanyoyi da aka samu.
Gidajen sarakai, Tarurruka misali irin taron yau na ranar mawaka na duniya. Sun hada da taron siyasa,
Taron biki ko suna, ko wani taro da ya shafi Sarauta da ma wanda bai shafi Sarauta ba. Kafofin yada labarai, Gidajen radiyo,talabijin,(social network) da sauransu. Bukukuwan Sallah. Gidajen gala

# TUBALIN GININ WAKOKIN FADA A YAU:

- Kamar yadda muka fada a baya turakun wakokin su ne dai a jiya kuma su ne a yau, don haka za mu dauki muhimman turakun mu kawo misali a kansu.

# KIRARI

Mudassir Kassim a wakarsa da ya yi wa marigayi sarkin Kano Alhaji Ado Bayero yana cewa:-

'Y/Amshi: Dan Bayero mai Kanon Dabo

Jagora: Riga ba ta san wuyan sawa ba sai a jikinka mai Kano Dabo,

- :Ba mai kudirin farar aniya Allah ya barka dan Abdu,
- :Hadari malafar gidan duniya,silken damarar zuwa yaki,
- :Ai kyawun da ya gaji uba,to kai gadon halin Abdu.



# Yabo

- Mawakan fada a yau sukan yabi Basaraken da za su yi wa waka da kalamai na yabawa da jinjina da kuzantawa.Misali Naziru M Ahmad a wakarsa ta "jikan Dabo" yana cewa:-
- Jagora: Ka ga maza ka shiga gurbin nema,
- :Ka zama kogi da ruwa ai wanka,
- :Rai nai ya dade rai ya dade Ado
-
- Bayero :Dan sarki da ruwan alfarma,
- :Ka ga kudi masu tukwicin nema,
- :Kai da ka taso baka san tsoro ba,
- :Karriki mai shi ba a ma wayo ba,
- :Kazzama Mahdi masshahurin sarki.
-
- Jagora:Mun ga ado mun ga ado Ado Bayaro,
- :Kai dawisu gidan mai dama,
- :Ka ga gida ka fa kudi mai dama.



# .....Yabo

- A wata wakar kuma da Naziru Ya yi wa mai martaba sarkin Kano Malam Sunusi Lamido ta "Mata ku dau turame" Inda yake cewa:-
- Jagora: Ku doka tamburan Alaraini,
- :Sarkin Kano matarar yaki,
- :Ga tsakin tama dan Audu,
- : i iimi ku ce insanu,
- :Ba aljan bare Ifritu,
- :Maza jiran maza dan Abdu,
- :Ko masu kin ka  sai sun soka..

# Tarihi

- Mawakan da suke yi wa sarakuna wakoki a yau suna amfani da tubalin tarihi wajen gina wakokin sarauta .Misali Amin Ladan Abubukar Alan waka a wakarsa ta Sarkin lafia, Alhaji Isa Mustafa Agwai yana cewa:
- Jagora: Na waigo da tarihin Elkanemi Barno ‘yamfaya,
- :Asalin mutan Yamen can Madina na Makiyya
- :Ga asalin Babebari tun daga Yamen har ga Lafiya,
- :Jinin Sultan Sa'f Aty sarki na Sana'a a tun jiya,
- :Mamman Ali Madu Ahmad jini Isa Agwai mazan jiya,
- :Mamman Ali Madu Ahmad jinni Isa Agwai mazan jiya,
- :Tun karni na sha bakwai zan bitar talifin mazan
- jiya,
- :Kawo har ishirin da daya zangin Isa Maliya,
- Allah kara lafia Isa Mustapha Agwai,
- :Mai nasabar gida Ali toron giwa ko na ce giye, :Allah kara lafiya ,Allah kara lafia.



# ZAMANTAKEWA

- Mawakan fada a yau su ma suna bayyana irin yadda sarakunansu ke da kyakkyawar zamantakewa da talakawansu, misali a wakar Sarkin fulanin Gombe mawakiya Aisha Umar tana cewa:-

- Jagora:Umaru Kwairanga dan baiwa wanda bai gudun al'umma don sun zo,
- :Jarumi mijin Gabaffa,
- :Umaru Kwairanga jarimunmu wanda ba ya gudun talakawa,
- :Shi ya sa yake da masoya ko'ina in ya fito ana ta lale marhabin barkama..

# ROKO

- Har a yau wadanda ke wa sarakuna waka suna amfani da kalmomin roko ga sarakunan da suke yi wa waka kamar yadda mawakan fada suke yi a jiya. Misali, Naziru M. Ahmad a wakarsa da ya yi wa sarkin Kano Muhammad Sunusi na biyu yana cewa:- Jagora: Da na ji gangunan sun tashi,
- : sai na kira yarima Ingawa,
- :Da na ji duniya ta dauke,
- :sai in kira yarima Ingawa,
- :Ruwan dala yana min dai-dai,
- :Wannan sagin ya nai don dan Lamido.

# KAYAN KIDAN MAWAKAN FADA A YAU

- Bahaushe ya ce "In kida ya sauya sai rawa ta canja" A nan waka ce ta sauya sai kida ya sami sauyi. Mawakan da ke yi wa sarakai waka a yau sun gwamutsa kayan kidansu na zamani da kuma kayan kidan mawwakan baka na gargajiya domin karawa wakar armashi. Misalin kayan kidan akwai:-
- Fiyano
- Kalangu
- Life band/police band
- Gurmi
- Kukuma

# Wasu daga cikin mawakanmu na zamani









# KAMMALAWA

- Kamar yadda aikin ya gabata, wannan takarda ta kalli muhimmin bangare ne na makadan fada in da ta kalli yadda makadan da wakokin suke a jiya da kuma yau.Makadan fada na jiya sun kaura na yau sune suke raye kuma su muke gani muke yi musu fatan zaman mudubi kuma kundin tarihi don na gobe su gani don haska rayuwa ta gaba, hakan kuwa ba zai tabbata ba sai na yau din sun kyautata kamar yadda na baya suka yi.

- Kome dan'adam ya ke son cin ribarsa sai ya kyautata shi, kyautatuwar adabi kuwa shi ne yin riko da addini da al'ada don gudun kaucewa. Makadan fada na jiya sun yi iyakar kokari sun rike al'adunsu kama daga sutura da muhallin rera wakar da ma abin da za su fada wato kayan cikin wakar duk suna taka-tsan-tsan.

- A baya mawakan fada za ka iske su mutane ne da suke da ilimin addini dai-dai gwargwado wannan tushe ne mai kyau. A yau ilimin boko ya samu ya zama mahadin rayuwa. Yana da kyau makadan fada a yau su zamana suna da ido a dukan ilimin biyu dai –dai bukata don ba wani abu da ke samun nasara da jahilci.

# ......KAMMALAWA

- Makadan fada na jiya kan rike sarki guda ya zama ubangidansu wannan ne ke ba su damar zurfafawa da bincike da sanin masarautar, haka jama'ar fada sukan saki jiki da su har su fada musu wani abu na daga sirrikan masarauta.Wannan salo ne mai kyau na samun waka da ke dauke da ilimi kan wannan masarauta da samun hujjoji abin dogaro wanda makadan fada a yau ya kamata su dauka ko da ba su rike sarki guda ba to ya zamana dai suna da gamsasshen tarihin masarautar.

- Makadan fada a jiya suna amfani da kalmomi na azanci da fasaha duk abin da za su fada yana da tushe ta haka ne ma suka taimaka wajen ciyar da harshen gaba.Wannan kokari na su ya kamata mawakan baka na yau su dauka su ma su dora domin raya wannan harshen na Hausa.

- Mawakan baka na zamani su dage kada bakin wuta ya mutu a hannunsu, su din ga karamci ga masarta da iyaye da kakanni. Yadda suka baiwa sauran bangarori muhimmanci wajen wakokinsu kamar wakokin fadakarwa da na siyasa da na bukukuwa da na soyayya, to wannan fagen ma na wakokin fada su raya shi su kyautata shi don raya al'adun Hausawa da masarautunsu.

# RATAYE NA 1

- Makadan Fada na Jiya
- Wakar Marigayi Musa Dankwairo, wakar Sardauna (Mai damararYaki Na Hassan)
- 
- Gimbiya kan ta ta taho nan, ta ga k'asak ka, ta ga abin ban-mamaki; Shugaban Senegal ya taho nan, ya ga k'asak ka, ya ga abin ban- mamaki;
- Shugaba Jori Hammani ya taho nan, ya ga k'asak ka, ya ga abin ban- mamaki;
- Limamin Madina ya taho nan, ya ga k'asak ka, ya ga abin ban- mamaki;
- En, an yi shirin tariya zak kyawo,
- Tun bisa hilin jirgin Sakkwato,
- Hab bisa garka tai, masabki,
- Masu dawakina sun jera,
- Hakimmai da kamfannai an jera benci-benci,
- Kananan motoci da manya, kowane an jera zak kyau,
- 'Yan doka da 'yan sanda an jera layi-layi,
- Jirgi ya zo ya aje ku,
- Kun shiga mota da kai da shi,
- Hak ka kai shi masauki nai,
- Shi kau sannan yai jawabi:
- 'Ahmadu ka cika kwazo kwarai,
- Allah dai ya yi ma albarka.
- Kowane dai yaz zo Sakkwato,
- Shi ka hwadi da baki nai,
- Da aikata alherin da ku ke yi Shehu ya na nan bai-- '
- Sai ya ce 'Shaihu ya na nan bai kau ba!'"



Imam of Medina at Sokoto

# MAKADAN FADA NA YAU

- BAKAN DABO TA AMINU LADAN ABUBAKAR ALAN WAKA
- Y/A:Bakan Dabo san Kano dan baiwa,
- :Dan Abdallah lafiya takawa.
- 
- Jagora:Dan Abdallah san Kano takawa,
- :Abin bugun gaban Kano da Kanawa,
- :Marmara kashin kasa dan baiwa
- :Bango ne majingina gun bawa,
- :Matokara ta masu san tasawa,
- :Jeji ka fice gaban shingewa,
- :Hadari sa gabanka ba a hanawa,
- :Madubin sarakuna na arewa,
- :Sha kallo da armashin dubawa,
- :Mai kallonka ba shi nuna gazawa,
- :Dan Bayero fahari ga Kanawa.
- 
- Y/A Bakan Dabo San Kano dan baiwa,
- :Dan Abdallah lafiya Takawa.
- 

# ......MAKADAN FADA NA YAU

- Jagora: Dan Abdallah gaida tilon sarki,
- :Ko taron sarakuna da saraki,
- :In ka fito cikinsu ba cika baki,
- :Komawa suke kamar 'yan tsaki,
- :Dagatai suke sukke in fa ga Takawa.
- 
- Y/Amshi:Bakan Dabo  San Kano dan baiwa,
- :Dan Abdallah lafiya Takawa.
- 
- Jagora:Bakan Dabo na kira shi barade,
- :Don aikinsa ne a yau ya karade,
- :Dan Abdallah hadimi mai lugude,
- :Da ayyuka na khairu duk ya karade,
- :Birnin Dabo lafiya daukawa.
- 
- Jagora:Dan Bayero kai daban a saraki,
- :Dubi shigarka na saka mana doki,
- :Sarki mai hawa na ban mamaki,
- :Al'amuranka kwai abin mamaki,
- :Mai daibe hason Kano da Kanawa

# ……MAKADAN FADA NA YAU

- Y/Amshi:Bakan Dabo San Kano dan baiwa,
- :Dan Abdallah lafiya Takawa.
- Jagora:Na nutsa bincike a harka tawa,
- :Na gaza tadda mai sarautar baiwa,
- : Mai mulki ya San Kano na Kanawa,
- :Mai tsari ya San Kano na Kanawa,
- :Ban isko ba San Kano dan baiwa.
-
- Y/Amshi:Sarkin nahiyar Kano mai girma,
- :Mutan garinka na ganinka da kima,
- :Makwabtansu na ganinka da kima,
- :Baki na na jahar Kano na yi ma,
- :Fatan kara lafiya a Kanawa.
-
- Y/Amshi:Bakan Dabo san Kano dan baiwa,
- :Dan Abdallah lafiya takawa.
-
- Jagora:Dattijai suna  Allah ya tsare ka,
- :Mattasa suna Allah kare ka,
- :'Yanmata suna Allah san barka,
- :'Yan yara suna Allah kiyaye ka,
- :Mai Kano lamarinka sai dai baiwa.
- Jagora:Farin gani abin fahar ga Kanawa,
- :Sha wake yabo kirarin baiwa,
- :Wakokinka sun wuce kirgawa,
- :Mai wasa ka sai fa ya dagewa,
- :In ko ya kiya ya yo dambarwa

# ......MAKADAN FADA NA YAU

- Jagora:Mai horo a bi Allahu buwayi,
- :A lafiya toya matsafan bayi,
- :A lafiya sarauki marrashin shayi,
- :Hadari sa gabanka ba wani shayi,
- :Gun hakuri damo a sanka da sanyi,
- :Mahassadanka sun gaza da bulayi,
- :Mai taimako gurin musulmin bayi,
- :Ka yi taka ka yi ta ragwayen bayi,
- :Sarki Alhaji da shi ka yi koyi,
- :Sarki Ussuman da shi ka yi koyi,
- :Sarki Innuwa da shi ka yi koyi.

- Y/Amshi:Bakan Dabo san Kano dan baiwa,
- Dan Abdallah lafiya takawa.





# RATAYE NA 2

## Jerin Sunayen wasu daga makadan fada jiya da yau

- Ibrahim Narambada
- Salihu Jankidi Rayawwa
- Abdurrahaman Sarkin Kotso
- Aliyu Dandawo Shuni
- Mamman Sarkin Taushin Katsina
- Saidu Faru
- Musa Dankwairo Maradun
- Dankyana Dadi Jibiya
- Bawa Gabci Abdu Kurna
- Ibrahim Gurso
- Abdu Inka Bakura
- Danbawa Kaura
- Dadi Dolen Maroki
- Husaini Sarkin Kotso
- Marafan Kidi Wanke
- Birgediya Tambai Gusau
- Abdu Farar Kasa Dankwairon Gombe
- Dandodo Alu Mai Taushi
- Aliyu Gadanga Gusau
- Aminu Ladan Abubakar
- Mudassir Kassim
- Naziru M Ahmad
- Maryam Fantimoti
- Bello Billy O
- Sadi Sidi Sharifai
- Danladin kima
- Ibrahim Ibrahim

# MANAZARTA


- A.M (2010) "*Al'adunSarauta a Qasar Hausa*"Takardar da Aka Gabatar Don Tattaunawa a TsakaninMalamai da Xalibai Don CikasaWaniVangarena Neman DigirinaUku a FanninAl'adunHausawa a SashenKoyar da HarsunanNijeriya,KanoJami'arBayero.
- Abbas,U.A (2008) "*Waqoqi a Finafinan Hausa*" A CikinAlgaita Journal of Current Reaserch in Hausa Studies Volume 1 Kano: Benchmark Publishers
- Adamu,J.S (2008) "*Habaici a ZamantakewarHausawa*" A CikinAlgaita Journal of Current Research in Hausa Studies,Department of Nigerian Languages Kano: Bayero University
- Alhassan,H.daWasu (1982) *ZamanHausawa*.Islamic Publications Bureau, Zariya.
- Ali,B.Y.(2013)*Faxakarwa a WaqoqinBakana Hausa naZamani a Kano*.KundinBincike Wanda Aka Gabatar a SashenKoyar da HarsunanNijeriya da KimiyyarHarshe,Jami'arBayero,KanoDominSamunDigirinaBiyu a FanninAdabin Hausa(M.A.Hausa)
- Bello,G(1976)*"YaboZuga da Zambo a*

# .....MANAZARTA


- *WakokinSarauta"* A cikin Studies For The Study Of Nigerian Languages.Kano: BayeroUniversity
- Dumfawa,AA(2010) *"DangantakarWaqoqin Hausa da Samari*: RashinSha'awakoRashinFahimta" A cikinHimma Journal of Contemporary Hausa Studies.Department of Nigerian Languages, Umaru Musa 'Yar'aduwa University, Katsina.
- Funtua, A.A ( 2010) *"SigoginWaqoqinSiyasana Hausa a Jamhuriya ta Uku*" A CikinHimma Journal Contemporary Hausa Studies.Department of Nigerian Languages Umaru Musa 'Yar'aduwa,KatsinawaqarSardaunan Gaya

# .....MANAZARTA


- Gusau,S.M(2002) "*Saqo a WaqoqinBaka: TsokaciKanTurke da Rabe-Rabensa*" A cikinTarinTakardun da Aka Gabatar a BabbanTaronQarawaJunaIlliminaBiyarKanHarshe da Adabi da al'adun Hausa a Jami'arBayero,Kano
- Gusau,S.M(2014)"*WaqarBakaBahaushiya*"TakardaWadda Aka Gabatar a JerinLaccocina Bayan SamunMatsayinFarfesa a Jami'arBayeroKano
- Ibrahim Sheme,*DandalinMakada* Da Mawaqa A Whatsapp
- Kafin-Hausa,A.U( 2002) "*Koma-baya a Waqoqin Hausa: WaqoqinSarauta*" A cikinTarinTakardun da aka Gabatar a BabbanTaronQarawaJunaIlliminaBiyarKanHarshe da Adabi da Al'adun Hausa a Jami'arBayero,Kano.
- *Qamusun Hausa* (2006) Na Cibiyar Harshen Nijeriya ,Kano: Jami'arBayero.
- Malumfashi,I da Ibrahim,N.M(2014) *Qamusun Karin Maganar Hausa*. Kano,Garkuwa Publications